# Lallai waɗannan biyun haramun ne ga mazan al'ummata, kuma halal ne ga matansu

Daga Aliyu ɗan Abu Ɗalib - Allah Ya yarda da shi - ya ce: Manzon Allah - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya riƙe alhariri da hagunsa, kuma zinare da damansa, sannan ya ɗaga hannayensa da su, sai ya ce: "Lallai waɗannan biyun haramun ne ga mazan al'ummata, kuma halal ne ga matansu".
[Ingantacce ne]

Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya riƙe wani tufafi na alhariri ko wani yanki daga gare shi, da hannunsa na hagu, kuma ya riƙe zinariya ta ado ko mai kama da ita, da hannunsa na dama, sannan ya ce: Lallai alhariri da zinariya, sanya su haramun ne akan maza, amma mata to su halal ne garesu.



النجاة الخيرية
ALNAJAT CHARITY
لجنة الدعوة الإلكترونية
EDC E-Da'wah Committee